SUNAN ABOKIN HULƊA	LAMBAR SHAIDAR ABOKIN HULƊA TA ACES

Haƙƙoƙi da Nauyin da ke Kanka Yayin da kake Samun Ayyukan da Ma'aikatar Rayuwar Gida da Al'umma da kuma Ma'aikatar Taimaka wa Masu Nakasa ta samar

Your Rights and Responsibilities When You Receive Services Offered by Home and Community Living Administration and Developmental Disabilities Administration

Ayyukan da ke Samuwa

Kana da damar zaɓe daga cikin ayyukan da kake da damar samu. Ayyukan kyauta ne. Ayyukan da Hukumar Rayuwar Gida da Al'umma da Hukumar Tallafa wa Masu Nakasa za su iya biya, ba lallai su iya taimakawa su biya maka duk buƙatunka ba.

HCLA da DDA suna aiwatar da ayyuka a:

- Gidan Iyali na Manya, Cibiyar Taimakon Rayuwa, Cibiyar Ingantattun Ayyuka, Cibiyar Kulawa ta Ma'aikatan Jinya, ICF/IDs, Gidan Abokin Zamantakewa, Gidan Rainon Yara, Gidan Zama na Yara mai Ma'aikata Masu Lasisi; Gidajen Rukunin DDA, Gidajen Horar da Rukunai; KO
- Gidan mutum na kansa. **Lura:** HCLA da DDA ba sa samar da ayyukan da aka biya na kulawa na musamman na awanni 24 kowacce rana a gidan mutum na kansa. Idan ana buƙatar kulawar awanni 24, sannan za a iya duba sauran zaɓuɓɓukan aiki.

Hukumar Yankinka game da Manajan Al'amarin Tsufa, Manajan Kayan Al'amarin DDA, Ƙwarrre a Fannin Bayar Kulawar Jinya, Ƙwararre a Bayar da Kulawa, Ƙwararre a Fannin Aikin Zamantakewa na Ayyukan Gida da Jama'a ko Manajan Al'amarin Asibitin Jinya na HCS ana kiransa da **manajan al'amar**i a wannan daftarin.

Haƙƙoƙinka

Kana da haƙƙin:

- A kula da kai bisa mutuntawa, girmamawa kuma ba tare da wariya ba;
- A kula maka da kayanka da girmamawa;
- Aikin haɗin gwiwa da ma'akacin lamarinka wurin tsara kulawa da kai;
- A sama maka tafinta a kyauta idan ba ka iya yi ko fahimtar Turanci dakyau;
- A adana bayananka a sirri a cikin iyakar doka da kuma tsarukan DSHS;
- Kar a tilasta maka amsa wata tambaya ko yin wani abu da ba ka son yi;
- Za a sanar da kai game da dukkan ayyukan da za ka samu sannan ka zaɓi ayyukan da kake buƙata da waɗanda ba ka buƙata;
- Za a sanar da kai a rubuce game da hukunce-hukuncen hukuma sannan za a turo kwafin taƙaitaccen rubutun tsarin yadda za a ba ka kulawa da tallafi;
- Ƙin amincewa da ayyuka;
- Zaɓa, kora, ko canja horarren ma'aikaci;
- Samu sakamakon binciken bin diddigin kowanne ma'aikacin da ka zaɓa;
- Yi magana da wani mai kula idan kai ko mai maka aiki bai amince ba;
- Shigar da ƙorafi ko damuwa a kowane lokaci game da yanayi ko aikin ma'aikacin da ke kan tsarin shirin kulawa da kai, tsarin kulawa, ayyuka, ko duk wani abu da baka gamsu dashi ba bisa tsarin gida da kuma anguwarku. Kana da damar shigar da ƙorafi ba tare da ɗaukar fansa ba. Za ka iya shigar da ƙorafi ko damuwa ta hanyar kiran 1-800-737-0617, aika imel ga grievances@dshs.wa.gov, ko tambayar kowanne ma'aikacin DDA ko HCLA game da bayanai kan yadda ake shigar da ƙorafi;
- Nemi zama da ma'aikata ko da kuwa ka shigar da ƙorafi;
- Yi ƙorafi ba tare da tsoron cutarwa ba ko da ka nemi zama don tattaunawa da ma'aikata;
- Yi magana da lauya ta hanyar kiran 1-888-201-1014; sannan
- Ba tare da cin zarafi ba, wofantarwa, amfani da kai bisa zalunci, ko kuma watsarwa ba. Don bayani kan waɗannan batutuwan, ziyarci: https://www.dshs.wa.gov/altsa/home-and-community-services/types-and-signs-abuse Idan ana cin zarafi, wofantarwa ko amfani da kai ko wani bisa zalunci, daure ka kira layin DHS na kyauta a 1-866 (End Harm) /1-866-363-4276 don magana da ma'aikacin da zai taimake ka.

Barcode label

16172

SUNAN ABOKIN HULƊA	LAMBAR SHAIDAR ABOKIN HULƊA TA ACES

Ayyukan da suka rataya a kanka

Aikin da ya rataya a kanka shi ne:

- Ka ba ma'aikacin lamarinka damar cikashe tambayoyinka aƙalla duk shekara a wurin da baka takura ba;
- Ba ma'aikacin lamarinka ya ga inda kake zama aƙalla sau ɗaya duk shekara;
- Ba mu isasshen bayani don cikashe tambayoyin da kuma taimaka mana wurin gudanar da tsarin kulawa da kai;
- Sanar da ma'aikacin lamarinka idan wani daban yana yanke hukunci kan al'amuran lafiya ko kuɗi gare ka;
- Shiga cikin cigaban kulawa da kai ko tsarin tallafi ko saka hannu a kai;
- Mayar da martani da kuma tattaunawa da ma'aikacin lamarinka lokaci bayan lokaci;
- Zaben yadda za a kula da lafiyarka;
- Zaben ƙwararren ma'aikaci;
- Sirranta bayanan bin diddigi a kan ma'aikaci;
- Fahimtar cewa ba za a biya ma'aikacinka na ayyuka ko awannin da ba a sa hannu a kai ba;
- Sanar da ma'akacin lamarinka idan kana da matsaloli da ma'aikacinka ko idan ba ka samun awannin da ma'aikacin yayi iƙirarin samarwa;
- Biyan ma'aikacinka duk wata idan kana taimakawa wurin biya don kulawa da kai;
- Samar da wuri aiki mai aminci;
- Kar ka yi wani abu wanda zai saka kowa a hatsari;
- Sanar da ma'aikacin lamarinka kafin ka fita, idan za ka fita wajen jihar Washington tare da mai ba ka kulawa na musamman; sannan kuma
- Sanar da ma'aikacin lamarinka idan akwai canji a:
  - ✓ Yanayin lafiyarka;
  - ✓ Taimakon da kake samu daga dangi, abokai, ko sauran hukumomi;
  - ✓ Yanayin wadatar kuɗinka;
  - ✓ Inda kake samun kulawa;
  - ✓ Inda kake zama a jihar Washington; ko
  - ✓ Inda kake zama – kake shirin komawa, yanzu kana zama a wajen jihar Washington.

Ayyukan Suka Rataya a Kan Ma'aikacin Lamarinka

Ma'aikacin lamarinka yana da alhakin:

- Ya yi harka da kai bisa mutumtawa da girmamawa;
- Ya adana sirrrinka;
- Sanar da kai abubuwan da HCLAda DDA za su iya yi maka da waɗanda ba za su iya yi maka ba;
- Samu bayanai daga kai ko wasu don amsa tambayoyin da za su bayyana matakin taimakonka sannan kuma su yanke shawara kan ayyukan da za ka iya zaba;
  - ✓ Tambayoyin za su ƙunshi inda kake da ƙarfi, iyakoki, manufofi, da kuma abubuwan da ka fi so;
  - ✓ Jarabawar za ta ƙunshi taimakon da kake samu ko za ka iya samu daga dangi ko wasu hukumomi da kuma yadda kake so a aiwatar da ayyuka;
- Taimaka maka wurin bunƙasa tsarin kulawa ko tsarin tallafi wanda ke magance taimako da kulawa ta musamman da kuma manufofi ka ƙashin kai, abubuwan da aka fi so, da kuma ra'ayoyi;
- Samu bayanai daga kai da wasu don sabunta tsarin kula da tsarin tallafi a kowacce shekara ko yayin da yanayinka ya canja;
- Ba ka isasshen lokaci don samar da bayanan da ake buƙata;
- Magance matsalolin tsarin kula ko kuma tsarin tallafi yayin da suka taso;
- Mutunta haƙƙoƙinka da kuma samar da ƙarin taimako wurin samun ayyuka idan kana da matsalolin lafiyar ƙwaƙwalwa, jijiyoyi, azanci ko kuma na zahiri; da kuma
- Taimaka maka wurin nemo ma'aikaci ƙwararre idan ba ka samu ba.

Barcode label

16172

SUNAN ABOKIN HULƊA	LAMBAR SHAIDAR ABOKIN HULƊA TA ACES

Buƙatu na shari'a

Kana da haƙƙin neman buƙatu na shari'a. Buƙatun shari'a za su iya ƙunsar abin da kake so ko damar mai shari'a a kan tsarin kulawa da lafiyarka. Buƙatun shari'a taƙaitaccen bayani ne game da abubuwan da kake so game da lafiya da/ ko kulawa da lafiyar ƙwaƙwalwa, tare da damar amincewa ko ƙin amincewa da magungunan lafiya, lafiyar ƙwaƙwalwa ko kuma tiyata, yayin da ba ka da kwanciyar hankalin da za ka iya yanke wannan hukuncin. Za ka iya janye buƙatunka na shari'a a duk lokacin da ka ga dama.

Aikin Rijistar Zaɓe

Dokar Rijistar Mai Zaɓe na Ƙasa ta 1993 na buƙatar dukkan jihohi su samar da taimakon rijistar zaɓe ta ofisoshin gwamnati. Amfani da rijista ko ƙin amincewa da yin rijista don zaɓe ba zai shafi ayyuka ko adadin alfanon da za ka samu ba daga wannan hukumar. Idan za ka so taimakawa wurin cike fom ɗin rijistar zaɓe, za mu taimaka maka. Za a ɓoye r'ayinka na yin rijista ko ƙin yin rijista kuma kawai za a yi amfani dashi ne don dalilin yin rijistar zaɓe. Idan ka yarda da cewa wani ya keta haƙƙinka na yin rijista ko na ƙin yin rijista, kana da haƙƙin a adana sirrinka kan yanke shawarar yin rijista ko wurin neman yin rijistar zaɓe, ko haƙƙinka ne zaɓen jam'iyyar siyasa ko kuma wasu ra'ayoyin siyasar da kafi so, za ka iya shigar da ƙorafi da:

Washington State Elections Office
PO Box 40229
Olympia WA 98504-0229
1-800-448-4881

Sa Hannunka

Sa hannu a ƙasa idan ka fahimci haƙƙoƙinka da nauyin da ke kanka kuma ka fahimci haƙƙopin da ke kan ma'aikacin lamarinka.

Sa hannun abokin cinikayya	Kwanan Wata
Sa Hannun Lauya	Kwanan Wata

Sanarwa don kwastomomi da masu ɗaukar aiki (Take na VI da VII), Jihar Washington Sashen Ayyukan Zamantakewa da Lafiya dama ce daidaitacciya ga masu ɗaukar aiki kuma ba ta bambanta wani sashi na aiki, shirye-shiryensu da ayyuka sun danganta ne da shekaru, jima'i, ra'ayin jima'i, jinsi, gane jinsi/bayyanawa, matsayin aure, launin fata, imani, launi, asalin ƙasa, addini ko ra'ayi, alaƙar siyasa, matsayi a soji, babban mai muƙami da aka sallama, Lokacin Vietnam, wanda bai daɗe da rabuwa ba ko wasu matsayi masu girma da ake karewa, kasancewa mai matsalar jijiya, ƙwaƙwalwa, nakasa ta zahiri ko amfani da kare ko wani mutum mai nakasa ya yi amfani da kare ko wani dabban da aka horar, biyan daidai ko bayanan jinsi.

Barcode label

16172

Haƙƙoƙi da Nauyin da ke Kanka Yayin da kake Samun Ayyukan da Ma’aikatar Rayuwar Gida da Al’umma da kuma Ma’aikatar Taimaka wa Masu Nakasa ta samar.

Dokokin Ma’aikatan Lamari

1. Yi bitar fom ɗin don amsa duk wasu tambayoyi game da haƙƙin abokan ciniki da nauyin da ke kansu. Yi bita tare da abokin ciniki a tambayoyin ainihin Kulawa (ko a wani Muhimmin Canji/ Duk shekara idan ba a saka hannu a fom ɗin ba). Idan aka samu sabon samfurin fom, tabbatar abokin ciniki ya sa hannu a sabon fom ɗin. Mafi sabunta na haƙƙoƙin abokin ciniki da nauyin da ke kansu wanda ma’aikacin lamarin ya gabatar kuma abokin cinikin ya sanya hannu ya maye gurbin fom ɗin da a baya aka saka hannu.
2. Tabbatar abokin ciniki ko wakilinsa ya sa hannu a kwafi biyu na fom don nuna cewa sun fahimci haƙƙoƙi da nauyin da ke kansu yayin samun ayyukan da Ma’aikatar Rayuwar Gida da Jama’a da kuma Ma’aikatar Tallafa wa Masu Nakasa take gabatarwa.
3. Shigar da kwafi ɗaya a rahoton abokin ciniki na kan na’ura sannan bayar da ɗayan kwafin ga abokin ciniki.